# Matsayin Wasali a Hanyar Rubutun Ajami

Rabi'u Muhammad Tahir
Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya da Afrika,
Jami'ar Ahmadu Bello Zaria

## Tsakure :

*Wasali a hanyar rubutun Ajami, abu ne da ke da muhimmancin gaske kusan sai da shi ake iya rabewa a tsakanin kalmomi masu kama dajuna, ke nan wasali zai iya zama wani jagora musamman ga mai koyo ko kuma gwani wajen iya karatun Ajami ko fahimtar kalmomi masu kamanni, duk da cewa wasu na ganin wasali a rubutun Ajami ba dole ba ne sai da larura, wannan ra'ayi ba ya ganin cewa wasali ya zama kamar wani sinadari ne a hanyar rubutun Ajami, wannan yajawo hankalin wannan makala da ta ce wani abu dangane da wasali a hanyar rubutun Ajami ta kuma yi kokarin bin tsarin wasali na boko domin a sami sauki wajen iya karatu da rubutu na Ajamin Hausa ta hanyar wasali. Saboda haka wasali a hanyar rubutun Ajami wata alama ce da ake amfani da ita wajen gane ko iya furta harafi ko kuma a iya fahimtar tagwayen kalmomi yayin karatu ko rubutun Ajamin Hausa, Zarruk (2000) ya bayyana wasali a hanyar rubutun Ajami da cewa wata alama ce da ake kestawa, a kasa ko sama da harafi a rubutun Ajami. Saboda haka wannan makala za ta bi tsarin wasalin Ingilishi, ta hanyar wasali a rubutun Ajami.*

## 1.0 Gabatarwa:

Duk Ajamin da aka tsara kuma aka rubuta shi bisa ƙa'idojin rubutu na Hausar Boko, kuma a kan hanyar Nazari, wannan shi ake kira daidaitaccen Ajami. Abin da ya sa aka daidaita ƙa'idojinsa da na rubutun boko kuwa shi ne. domin rubutun Boko na Hausa ko na Ingilishi ya samu tagomashi tun daga hannun turawan mulki har ya zuwa yau. Haka kuma waɗannan ƙa'idojin sun samu kafuwa da ƙarɓuwa, da kuma yaɗuwa ta hanyar samar da littattafan hira da jaridu da allunan tallace-tallace a gefen hanya, da kuɗaɗen Nijeriya. Wannan shi ya taimaka aka saba da waɗancan ƙa'idoji na hanyar rubutun boko. Saboda haka idan za a daidaita rubutun Ajami, kamar yadda wannan hanyar rubutu ta Boko ta samu, shi ma Ajami da ya yi sauƙi ainun wajen karantawa ko rubutawa. Hakan ya zama wajibi musamman idan aka tuna.

"wannan hanyar rubutu ta taimaka, lokacin jihadin Shehu Usman Ɗan fodiyo, wajen isar da saƙon malaman jihadi wajen yaɗa manufofinsu na jihadi,"(Jibril 2006: 9) .

Haka kuma: "rubutun Ajami ba na kowa ba ne, illa na Bahaushe, domin Bahaushe bai fara rubutu ba sai da Ajami". (Zarruƙ 2000)

Haka: " Ajami daɗaɗɗiyar hanya ce ta rubutu da haruffan Larabci ga jama'ar Afirika, wadda suke rubuta harshensu da ita..." (Ngom 2008).

Idan har sabawa da ƙa'idojin rubutun boko ya haifar sauƙaƙe karatu da rubutu na boko, ashe kuwa Ajami ya fi kyautatuwa da ya bi salon rubutun boko don samun sauƙin karantawa da rubutawa kamar yadda wannan maƙala za ta bi salon wasulan boko don sauƙaƙa karatu da rubutu na Ajamin Hausa. Hakan ya jawo hankalin maƙalar da fara tunanin cewa a rubutun Ajami ta fuskar wasali akwai wasula guda biyar kamar yadda ake da su a hanyar wasali na boko:

- a .........أ
- i...........إ
- o........ وْ
- u.........أُ
- e.......... اى

## 2.0 Ma'anar Wasali :

Wasali wata alama ce da ke zuwa tare da harafi a rubutun Ajami, walau a sama ko a ƙasa kamar haka (أإا) . Wasali ke mai da harafi ya tashi daga sunansa na harafi ya koma kalma daga nan kuma a sami jumla, sannan kuma wasali kan sanya baƙi ya canza, dangane da irin wasalin da ke tare da shi. Haka kuma wasali ke iya sa a bambance tsakanin kalmomi masu kama da juna:

- taushe........تَوْشي
- tushe..........تُوشي
- toshe..........تَوْشي

Idan aka dubi waɗannan misalai za a fahimci cewa waɗannan kalmomi ne iri ɗaya a wajen rubutu, amma kasancewa wasali a muhallin da ya dace a kan kowanne, sai hakan ya bambanta tsakanin waɗannan kalmomi.

Saboda haka muna da wasula guda biyar a hanyar rubutun Ajami:

* wasali sama: shi ne wasali wanda ake ƙestawa a saman harafi kamar haka ا wanda ake kira da wasali sama watau (a) yana iya kasancewa a kan kowane harafi misali:

  مَا .........م da wasali sama = m + a = ma
  جَ.........ج da wasali sama = j + a = ja
  دَ .........د da wasali sama = d+ a = da

* wasali ƙasa: wani ƙestu ne da ake aiwatar da shi a ƙasan harafi, a lokacin da ake rubutun Ajami don a iya furta wannan harafi yadda ya dace a hanyar rubutun Ajami yakan zo a ƙasan harafi kamar haka (!) a hanyar rubutun boko kuwa ita ce (i) misali:

  وِ...........و da wasali ƙasa = w + i = wi
  نِ..........ن da wasali ƙasa = n + i = ni
  كِ..........ك da wasali ƙasa = k + i = ki

* rufu'a: alama ce ta wasali wadda ake amfani da ita wajen iya furta harafin da ke ɗauke da ita ga yadda ta ke a hanyar rubutun Ajami (ُ) idan ta zo a kan harafi ga yadda take ٱ a wasalin boko kuwa ga yadda take (u) ga misali a hanyar rubutun Ajami:

  شُ...........شُ da rufu'a = sh + u = shu
  سُ...........سُ da rufu'a = s + u = su
  لُ.............لُ da rufu'a = l + u = lu

* wasalin (e) wani nau'i ne na wasali wanda ake amfani da shi wajen rubutun Ajamin Hausa, sai dai a wannan ɓangare za a fahimci cewa haruffa ne a matsayin wasali, kamar haka يا wanda a rubutun boko yake matsayin (e), amma a hanyar rubutun Ajami wasalin (e) ba ya zuwa a sama ko a ƙasan harafi a'a yakan zo ne tare da harafi wani likaci kuma yakan zo ne kusa da harafi ma'ana ya ce da alu-ja a sama, duk inda aka ga

ya ta zo ɗauke da alu-ja a samanta ko kuma suka zo tare, wannan harafi za a karanta shi ne da wasalin (e) a hanyar rubutun Ajami:

يـِي..............يي da wasalin e = y + e = ye
شـِي...........شي da wasalin e = sh + e = she
ثـِي........... ثي da wasalin e = c + e = ce

* wasalin (o) yana ɗaya daga cikin wasullan da ake iya amfani da su wajen abin da ya shafi wasalin (o) a hanyar rubutun Ajami, sai dai a tsarin wasalin (o) a hanyar Rubutun Ajami ana amfani da wau (وْ) amma da ɗauri a sama wanda ke nuna cewa wannan wasali ne na (o) a hanyar rubutun Ajami, idan an sami wani harafi ya biyo bayan (وْ) wau da ɗauri, sannan harafin ba shi da wani wasali a samansa, to wannan wau da ɗauri shi ne wasalin (o), idan kuwa harafin da ke biye da wau yana da wasali a samansa, wannan wau da ɗauri ba wasalin ba ne, misali kalmomi masu wasalin (o) a hanyar rubutun Ajami:

نوْ ........................no
كوْ........................ko
سوْ........................so

Idan an dubi misalan da ke sama za a gane cewa harafin da ke biye da wau mai ɗauri babu wani wasali a samansa, idan kuwa za a sanya wasali a saman harafin da yake biye da wau mai ɗauri a sama, ya tashi a matsayin wasalin (o) ya koma ɗauri ga misali:

نَوْ..........................nau
كَوْ..........................kau
سَوْ.........................sau

Daga misalin da ya gabata za a fahinci ma'anar ta sauya, sannan kuma yanayin rubutun ya canza daga wasalin (o) ya koma ɗauri saboda zuwan wasali a kan harafin da ke biye da wau.

Saboda haka wannan ya sa maƙalar ke ganin, Ajami yana da wasali guda biyar kamar yadda rubutun boko yake da su masu siga ta ma'ana kamar haka:

| | | | | |
|---|---|---|---|---|
| e =ای | U =اُ | o = وْ | i =اِ | a =اَ |

Ko da yake wasali a hanyar rubutun Ajami abu ne wanda ya sha bamban da wasali a hanyar rubutun Larabci, domin a Larabci suna amfani da faɗuwa a hanyar rubutunsu, wanda yake yin haka a hanyar rubutun Ajami kure ne, wannan ta ya haifar da ware wasu daga cikin wasullan Larabci ba a amfani da su a hanyar rubutun Ajami kamar haka:

**Wasulan da aka Watsar**

| | |
|---|---|
| Fatahatain | اً |
| Kisratain | اٍ |
| Dammatain | اٌ |

Saboda haka waɗannan su ne, wasula ko kuma faɗuwa watau wasula biyu a ƙasa ko a sama, waɗanda ba su da wani gurbi a hanyar rubutun Ajamin Hausa. Saboda haka ga misalin su ta hanyar rubutu kamar haka:

| Daidai | Kuskure |
|---|---|
| تَمَانِنْ | ثَمَانٍ |
| مَاشِنْ | مَاشٍ |
| دَبَنْ | دَبٌ |
| تَمَانِنْ | ثَمَانٍ |

Har ila yau a hanyar rubutun Ajami akwai musayar faɗuwa na wasullan Larabci, idan dai mai rubutu na Ajami zai yi amfani da kalmar da take da sauti kamar na faɗuwa a rubutunsa, sai dai ya yi amfani da waɗannan a matsayin waɗancan kamar haka:

| | |
|---|---|
| An | اَنْ |
| In | اِنْ |
| Un | اُنْ |
| | |

Daga misali na sama na farko wanda ke nuna musayar faɗuwa ta Larabci kamar haka (اً) wadda a hanyar wasali na Ajami ba haka ake rubutu ta ba, sai dai a rubuta kamar haka (اَنْ) ta yin amfani da alu mai wasali sama sannan ya ɗauri nu'ara a matsayin 'an' ke nan, haka kuma idan misalin da ke biye da wannan ne kusan haka abin yake, sai dai canjin wasali walau a ƙasa ko kuma akasin haka. Don haka ga misalin yadda faɗuwa take a kalmomi ɗomin iya tantancewa:

| Hausa | Daidai | Kuskure |
|---|---|---|
| an sauya | أنْ سوْيا | اَ سوْيا |
| an ɗura | أنْ طُورَا | اَطُورَا |
| an surka | اَنْ سُر كا | اَ سُرْكاَ |
| an tsara | اَنْ ظَار | اَ ظَار |

Idan an lura da misalan da aka gabatar dangane da faɗuwa a tsarin wasalin Larabci, za a fahinci cewa faɗuwa a tsarin rubutu na wasali ta hanyar Ajami ba shi da wani muhalli, kamar yadda bayani da misali suka gabata, watau wasali biyu a sama َ ko a ƙasa ِ ko kuma a kowane muhalli ne na rubutu na tsarin wasali a hanyar Ajamin Huasa.

### 3.0 Auren Wasali :

Auren wasali a rubutun Ajami shi ne ɗaurin da wasali ke yi ma harafi, wasali ne ɗaya zai auri haruffa guda biyu a lokaci guda, ko kuma wasali ne ke wakana a kan harafin farko sannan kuma sai wani harafin mai biye masa ya kasance da ɗauri, wannan shi ne auren wasali a rubutun Ajamin Hausa, duk da cewa a rubutun Boko ba haka abin yake ba, wasali ne ke auren wasali, amma hanyar rubutun Ajami harka ce ta wasali da harafi a lokaci guda a matsayin auren wasali. saboda haka za a iya cewa haruffa ne ke haɗuwa wuri guda sai wasali ya aure su, domin su ba da abin da ake buƙata misali:

au -اوْ ai -اىْ

Daga misalin da ya gabata za a iya fahimtar cewa, auren wasali a rubutun Ajami da kuma Boko ababe ne mabambanta, domin a rubutun boko wasulla ne guda biyu ke haifar da auren wasali, saɓanin auren wasali a rubutun Ajami, inda haruffa ne ke haɗuwa sai wasali na sama ya ɗaure su. Har ila yau za a iya cewa ke nan, auren wasali a rubutun Ajami ɗaurin da wasali ke yi wa harafi ne ke haifar da aure, idan aka dubi misalin da ya gabata za fahinci haka.

**Wasalin** 'اوْ'

مَوْ نَوْ سَوْ
دَوْ ثَوْ گَوْ
شَوْ طَوْ رَوْ

Saboda haka daga misalin da aka gani a sama, za a fahinci cewa wasalin au a rubutun Ajami yana tafiya ne, da harafin , 'و' bayan alu baƙi da wasali sama ya gabace shi a kowane lokaci, ta wannan hanyar ce suka bambanta da rubutun boko, kuma shi ya sa kowane harafi aka aura sai a ga harafin 'و' a ƙarshen harafin da ya yi ɗauri wanda hakan shi ne auren wasalin (au) ta hanyar rubutun Ajami, kamar yadda bayani ya gabata.

Wasalin 'اَیْ'

Wasalin 'اَیْ' ko da yaushe yakan zo da 'ی' ma'ana yana bin harafin da aka aura,watau alu baƙi ya auri ya auri (y) kamar haka 'اَیْ' wannan shi ke bayyana auren wasali na na (aî) a hanyar rubutun Ajami kamar haka 'اَیْ'. Saboda haka ga misalin auren wasali na 'اَیْ' a cikin kalmomin Ajami kamar haka:

| | | |
|---|---|---|
| وَيْ | سَيْ | مَيْ |
| شَيْ | ذَيْ | جَيْ |
| زَيْ | هَيْ | ݣَيْ |

## 4.0 Muhimmancin Wasali a Rubutun Ajami :

Wasali wani kaɓaki ne babba wanda ke iya gamsar da mai karatu wajen iya tantance tsakuwa da tsaba a tsakanin haruffa da kuma jerin wasulla a hnayar rubutun Ajami. Har ila yau wasali ne kaɗai ke iya bambance tsakanin tagwayen kalmomi a rubutun Ajami misali:

| | |
|---|---|
| bauta | بَوتَا |
| bota | بوْتَا |
| buta | بُوتَا |
| kora | كوْرَ |
| kaura | ݣَوْرَ |
| kura | ݣور |
| kauru | ݣَوْرُ |

idan aka dubi yadda waɗannan kalmomi suka ksance, za a fahinci kalmomi ne tagwaye babu wani abu da ya bambanta su sai wasali, idan a n zo furta su amma idan aka ɗebe wasalin da ke kan waɗannan kalmomi, mai karatu zai karanta su ne, a matsayin abu ɗaya sai dai wanzuwar wasali ya tsakanin zare da abawa. Haka kuma yana daga cikin muhimmancin wasali a rubutun Ajami, ya nuna wa mai karatu matsayin harafin da ke ɗauke da shi.

| | |
|---|---|
| saura | سَوْرَ |
| sauri | سَوْرِ |

Dangane da misaalan da aka gabatar a sama, za a fahinci cewa kalma ta farko tana da wasali, kalma ta biyu kuma tnaa da wasali,sai dai abin da bambanta su shi ne kasancewar kowane wasali a muhallinsa, haka ne kaɗai ya iya tantance tsakanin haruffan da aka yi amfani da su, domin idan an dubi haruffa za a ga ne cewa kusan suna da kamanni da juna ta fuskar rubutu amma wajen furucinsu sun bambanta, saboda muhimmancin da wasali yake da a wasu gurabu a hanyar rubutun Ajamin Hausa. Har wa yau wasali ke iya tantance tsakanin wasalin 'وْ ' watau (o) da kuma ɗauri. Sau da yawa mai karatu na ɗaukar wasalin 'وْ' da ɗauri a matsayin abu ɗaya. Saboda haka ga misalin wasalin 'وْ' a cikin kalma.

| | | |
|---|---|---|
| سوْيَ | . | soya |
| روْبَ | | roba |
| دوْيَ | | doya |
| توْيَ | | toya |

Daga misalin da aka gabatar a sama, za a ga cewa akwai alamar kamar ɗauri a kan '0' wau wadda take nuna cewa wannan wasali ne, na 'وْ' a rubutun Ajami ba ɗauri ba, amma haka yakan faru ne, idan harafin da ya fara zuwa kafin 'و 'ba shi da wani wasali, ko da yake a ƙa'idar rubutu na Ajami a wajen rubuta wasalin (o) harafin da ya gabaci 'و ' ba ya zuwa da wani wasali a sama, idan kuwa har ya zo da wasali a samasa to wannan harafin ba mai ɗauri ba wasalin (o) ba ne ɗauri ne, amma idan mai rubutu ya rubuta haka ' سَوْيَ' watau sin da wasali sama ta ɗauri wau, kasancewar haka wannan wau mai ɗauri tun da sin ta zo da wasali sama ya tashi a matsayin wasalin (o) ya koma ɗauri, domin harafi 'س' yana da wasali a samansa, wannan ne ya sa kalmar ta tashi daga 'soya' ta koma 'sauya'.

## 5.0 Kammalawa :

Wasali wani tsani ne, da ake iya hango daidaituwar dangantakar wasali da kuma harafi, sannan ta hakan ne, za a iya sauƙaƙa wa ɗan koyo ya iya karanta rubutun Ajami cikin sauƙi. don haka ne aka bayyana matsayin wasali a rubutun Ajami, tun daga yadda aka kawo wasullan da ba a amfani da su, wajen rubutun Ajami. Sannan kusan a iya cewa wasali shi ne, jagoran da ke iya kai mai karatu ga tudun mun tsira a yayin karatun Ajamin Hausa, haka kuma shi ke iya kwance tarnaƙin da ke dabaibaye da tagwayen kalmomi a rubutun Ajami don a iya tantance tsakanin wajen karatu ko rubutu. Hakan ke ba da damar ga ne tsakanin wasalin 'o' da kuma ɗauri, kuma wasali ke sauya wa kalma ma'ana nan take don muhimmancinsa a rubutun Ajami. Sau da yawa rashin wasali ga mai koyon karatun Ajami, kan haifar da ruɗu da ruɗani kai har ma da ƙosawa.

## Manazarta

Binji, H da Wali, N.S. (1990) *Mu koyi Ajami da Larabci,* NNPC Zariya.

Birnin Tudu, S.Y.(1990) *Nazari kan Rubutun Ajami a ƙasar Hausa* Takardar da aka gabatar a taron bitar da Cibiyar Nazarin Addinin Musulunci ta Jami'ar Usmanu Ɗanfodoyi Sokoto.

Bunza, A.M. (2009) *Ajami Heritage:* (*Its Role and Relevance in the Preservation and Conservation of Hausa Literary Art and Culture*) paper presented at the international conference on Exploring Nigeria's Arabic/Ajami Manuscript Resources for the Development of Knowledge Organized by Arewa House, Kaduna

Bunza, A.M. (2007) *Kundi Book legacy in pre-colonial Hausa.* paper presented at two days international conference on preserving Nigeria's Scholarly and literary Traditions and Manuscripts, Arewa House, Centre for Historical Documentation and Research, Ahmadu Bello University, Zaria, in Collaboration with the United State Embassy Abuja.

Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya (2009) *Tarihin Ajamin Hausa Kafin Jihadin Shehu Usmanu Ɗanfodiyo.* Taron Karawa da sani 27-30 Disamba, 1989 Jami'ar Bayero Kano

Gumi, A.M. (1982): *Alkur'ani Mai Girma.* Tarjamar Ma'anoninsa; Dar al Arabia, Lebanon.

Greenberg, J.H. (1947). *Arabic Loanwords in Hausa* WORD iii .

Gwandu, A.A. (2009) *Exploring Nigeria's Arabic/ Ajami manuscripts heritage in Nigeria.* Maƙalar da aka gabatar a taron ƙara wa juna sani. Gidan Arewa da adana tarihi Jami'ar Ahmadu Bello Zariya.

Gwandu, A.A. (2008) *Transliteration of Arabic into Hausa characters.* Maƙalar da aka gabatar a taron ƙara wa juna sani. Cibiyar nazarin addinin muslunci. Jami'ar Usmanu Ɗanfodiyo sokoto.

Hunwick, J. (1977) *The Arabic Literary Translation in Nigeria.* Research in African literatures. P.210

Junaidau, I.S. (2008) *Harshen Fulani a cikin haruffan Larabci (Ajami)* babu inda aka gabatar.

Jibril, U.F. (2006) '*Community Mobilazation in Traditional Societies: A contextual Appraisal of the Role of Oramedia in the 1804 Uthman Dan fodio Jihad Movement*'. P.6 Maƙalar da aka gabatar a taron ƙara wa juna sani. Jami'ar Bayero Kano

Mukhtar, A.Y. (2008) *Ajami: samuwarsa da bunƙasarsa a ƙasar Hausa.* Algaita Journal of current Research in Hausa Studies, Vol, 1 No. 5 Satumba.

Mohiyidin, B.A. (1981) *Islamic Religious Studies History,* 1st Ed. India: Continental Book Centre , p.29

Ngom, (2008) *Ajami the Interlectual Heritage Wikipedia free encyclopedia*

Report on Hausa ajami writing (1988) *Center for Islamic studies,* Usmanu Danfodiyo University, Sokoto

Umar, I.W. (1989) *Amfanin Rubutun Ajamin Hausa, Ka'idojinsa da Matsalolinsa.* Taron Karawa da Sani 27-30 Disamba, A Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya. Jami'ar Bayero Kano

Yahaya , I.Y. (1988). *Hausa a rubuce tarihin rubuce- rubuce cikin Hausa.* Zaria. Gaskiya Co'operation Limited

Zarruƙ (1980) *koya wa kanka ajami.* Institute of education Ahmadu Bello University, Zaria

**Hira:**

Zarruƙ, R.M. (2000) Ma'a *nar Ajami* , Institute of Education Ahmadu Bello University Zariya

Junaidau, I.S. (2008) *Harshen Fulani a cikin haruffan Larabci (Ajami)* babu inda aka gabatar.

Jibril, U.F. (2006) '*Community Mobilazation in Traditional Societies: A contextual Appraisal of the Role of Oramedia in the 1804 Uthman Dan fodio Jihad Movement*'. P.6 Maƙalar da aka gabatar a taron ƙara wa juna sani. Jami'ar Bayero Kano

Mukhtar, A.Y. (2008) *Ajami: samuwarsa da bunƙasarsa a ƙasar Hausa.* Algaita Journal of current Research in Hausa Studies, Vol, 1 No. 5 Satumba.

Mohiyidin, B.A. (1981) *Islamic Religious Studies History*, 1st Ed. India: Continental Book Centre , p.29

Ngom, (2008) *Ajami the Interlectual Heritage Wikipedia free encyclopedia*

Report on Hausa ajami writing (1988) *Center for Islamic studies*, Usmanu Ɗanfodiyo University, Sokoto

Umar, I.W. (1989) *Amfanin Rubutun Ajamin Hausa, Ka'idojinsa da Matsalolinsa.* Taron Karawa da Sani 27-30 Disamba, A Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya. Jami'ar Bayero Kano

Yahaya , I.Y. (1988). *Hausa a rubuce tarihin rubuce- rubuce cikin Hausa.* Zaria. Gaskiya Co'operation Limited

Zarruƙ (1980) *koya wa kanka ajami.* Institute of education Ahmadu Bello University, Zaria

**Hira:**

Zarruƙ, R.M. (2000) Ma'a *nar Ajami* , Institute of Education Ahmadu Bello University Zariya